INT. DR. GIREMA -CONTINUOUS

Fa'iza da Laraba suka shigo.

FA'IZA
Salamu alaikum

Ta ja gefe ta tsaya. Safara'u ta karasa gaban teburin Dr. Girema.

**LARABA**
Barka da aiki Malama.

Malam Juwairiyya ta nuna wa Safara'u kujerar zama fuskarta babu walwala.

DR. GIREMA
Zauna mana.

Safara'u ta zauna ta fuskance ta, za a ga hankalinta duk a tashe.

Dr. Girema ta dubi safara'u da kyau.

DR. GIREMA (CONT'D)
Malama Safara'u ba ki taba kawo kudin tara ba.

**LARABA**
(da yanayin rashin sani)
Malama tarar me fa?

DR. GIREMA
Kin manta? to bari in tuna miki. kwanakin baya na tara ku na sanar da ku cewa idan daliba sun yi laifi, a daina ba su gwale-gwale, a dinga yanka musu tara.

Safara'u ta yi kasake alamar rashin abin cewa. Fa'iza da Malama Girema suka kakkafe ta da ido.

**LARABA**
(tana in'ina)
Yan ajina ba sa laifi Malama...

FA'IZA
(ta zaro ido)
La ila!

Sai kuma ta yi shiru da sauri ta ha hannu ta rufe baki. Malama da Safara'u duk suka kalle ta.

DR. GIREMA
Fadi abinda kike son fada Malama Jamila.

FA'IZA
Gaskiyar magana Malama duk makarantar nan babu ajin da ya kai ajinta kangararru, sai dai idan karba ta ke ba ta kawowa...

Ta kalli Fa'iza cikin kaduwa.

**LARABA**
Na rantse da Allah ban taba karbar ko sisi ba, idan ba ki yarda ba ma sai in je in dauko rasit din ki gani, ban taba yagar ko daya ba...

Fa'iza tana satar kallon idon Dr. Girema tana nuna mata alamar cewa karya Safara'u ta ke.

DR. GIREMA
Idan kuma kin karbi kudin baki rubuta rasit ba fa?

Safara'u ta yi shiru cikin damuwa.

DR. GIREMA (CONT'D)
Ya zama lallai ki dinga kawo wa kamar yadda yan'uwanki Malamai ke kawo wa.
(ta nuna Fa'iza)
Ita yar uwarki da yake mutuniyar kirki ce tana kawo nata.

**LARABA**
(a tsorace)
Ni karbar kudin ne na ke ganin kamar ba hanyar gyaran hali ba ce malama...

DR. GIREMA
(a fusace)
Shawara na tambaye ki kuma kiranki na yi na sanar da ke dokokin makaranta ta? Ke me kika sani akan wani gyaran hali da za ki yi mana tsari!?

**LARABA**
(da yanayin nadama)
Ba haka nake nufi ba, ki yi hakuri Malama...

DR. GIREMA
Karbar kudin tara ka'idar da makaranta ta gindaya kenan babu wanda kika fi zane, saboda haka ki je ki dinga kawo tara kamar yadda kowa ke kawowa.

**LARABA**
(tana ta kada kai)

To shikenan Malama.

DR. GIREMA
Shikenan tashi ki je.

Safara'u ta mike jikinta a sanyaye ta fita. Tana fita Fa'iza ta taho kujerar da ta tashi da sauri ta zauna.

FA'IZA
Na rantse da Allah da Annabi Malama karya ta ke, Munafuka ce.

DR. GIREMA
(tana gyada kai)
Na fahimci haka!

FADE OUT.